[16/01, 18:47] khadija ahmad dija Marubuciya Barauniya ce Frien Din Hassn: ✨ba don shiba✨
By Princes Deejerh
New Writer

Bismillahir rahmanir raheem
Page1️⃣to5️⃣

yarinya ce yar kimamin shekara 14 take ta kai kawo a cikin tsakar gidan kallo daya zaka mata zaka gane agalaibe take aikin juyar da kanta tayi zuwa wani sashe dake tsakar hmm tace a hankali nima na kai dubana sashen da take kalla abin mamaki wani uban tulin kayan wanke wankene kamar anyi sati ana tara shi kuda kuwa sai rawar banjo suke akai hawaye ta share a hankali kafin ta doki kujera yar tsugunne ta karasa wurin zama tayi jiki a sanyaye ta fara wankewa dama ta riga ta dibo ruwan tunda safe kanta a duke yake amma duk hakan bai hana hango hawayen da ke zuba a idonta ba wata irin rayuwa akeyi a gidansu ta rashin adalci akwai yayyanta yanmata har gudu uku amma basa aikin komai sai dai kawai ayi kwalliya a fita harta kayansu ita ke wanke tana cikin wannan tunanin bata auneba taji wani uban rankawashi akanta kwass kake ni kaina sai da na tsorata dago kai tayi da sauri tana shafa gurin domin ba karamin shigarta rankwashin yayi cikin rawar murya tace ki..kiyi hakuri inna mtsww dogon tsakin da matar taja ne yasa na daga kai na kallet kibarta sai data tsora tani ga idonta manya2 bakin wargajeje duk ya baci da goro kannan kuwa dukun dukun yake kamar an shekara baa kitsa shiba hargowan da takeyi ne ya bani dama hango wawake ken wuwulon dake bakin kai wannan mata ta cika kazama cigaba tayi da masifa tana fadin shegiyar yarinya me bakin halin ubanta tun dazu na saki aiki amma kina nan kina halin na munafunci ta kara kai mata duka a baya wallahi ba zaki makarantar da ake koyo miki iskanci ba bari haladu ya zo yau sai kinfi fulawa laushi kuma ki gama ga wankinsu indo can kije ki wanke su tass tunda anhana kimin tallah aikin gida ma kawai ya isheki shegia mai kama da mayu infito inga baki gama ba tunda ta fara fadanta bata dago ta kalleta ba domin kuwa tasan me hakan zai haifar mata hawayen fuskarta ta share amma kuma wasu kara zubowa suke ba duka ko zagin a akai mata bane damuwarta ta riga ta saba duk da baa sabo da wahala makarantar ta shine damuwarta domin kuwa yau suna da test kuma wannan year din zatai junior waec da sauri sauri ta kama aikinta da yake me kwazo tuni ta gama shi mikewa tayi a hankali ta leka dakin inna asabe munsharin da take ne ya tabbatar datayi bacci da gudu ta shige dakinsu ta dakko uniform dinta kayan tsab domin kuwa a goge suke komai da sauri take yinsa saboda kada inna ta tashi bata dauki jaka ba littafi kawai ta dauka sai biro fitowa tayi fice a gidan a hankali tafiya take cikin nutsuwa duk da kuwa tasan tayi latti wannan nature dinta ne duk napep din data tara a cike suke saboda yau safiyar monday ce dakyar ta sami wani mai mashin ya tsaya mallam gumi college zaka kaini tun kafin ta gama rufe baki yace 200 zaro ido tayi ita da take naira 30 shiru tayi domin tasan ba kaita zaiyi ba dan baida alamun mutunci a hankali tace muje to (nidae nace to waye zai biya ta taro pillars) yan mintoci kadan sukai kaisu bakin makarantar  sauka tayi tare da sunkuyar dakai gajiya yayi yace yadai malama kudinafa zan baka tace a hankali
acan gefen kuma wani saurayi na hango zaune a bakin get din makarantar kanshi a duke yake amma haka bai hanani gano baiwar kyau dake kunshe a fuskar sa ba tsayawar mashin diinne yasa shi dago kanshi da sauri masha allah na fada saboda duk inda ake neman mai kyau to

wannan guy din ya wuce idanuwan shi manya ne farare tass hancinshi dogo har baka bakin dan mitsili pink dasu mikewa yayi ransa a bace takowa yayi har inda me mashin din yake hararar sa yayi kafin  ya ciro kudi ya mika ma dan acaban wuce muje yace mata sai da suka kai bakin ajinsu yace waya ce ki hau mashin turo baki tayi tace to ban samu abin hawa bane ne ai mtsw yayi tsaki kafin yace ya akayi kikayi latti shiru tyi ke dallah kimin magana wanki nayi wankin wa nasu indo mtsw sai naci uwarsu duka yasin wannan tsohuwar kuma inbata yi a hankali ba sai na cire mata murfin kai ya fada yana wani karkta baki kallon shi tayi a tsorace domin kuwa tasan zai iya indai AMMAR ne wuce aji kin wani tsaya kallo na wucewa tayi da murmushi a fuskarta har tayi nisa ya kwala mata kira JIDDAH waigowa tayi  zonan yace da sauri ta taho kudi ya ciro ya mika mata ba musu ta amsa nagode hararar ta yayi hmm tace dan tasan manufar hakan baayaso tamai godiya wucewa duka suka yi kowa yayi ajin shi

Princes Deejerh💝
[16/01, 18:47] khadija ahmad dija Marubuciya Barauniya ce Frien Din Hassn: ✨✨BA DON SHIBA✨✨

by Princess Deejerh
 New Writer

Page6️⃣to1️⃣0️⃣

shigarta cikin aji yayi daidai da zuwan teacher din su na english dama shine 1s test da zasu fara,ba bata lokaci ya fara rubuta musu test kan ka ce me har jidda ta kusa gama nata domin kuma jidda akwai kwakwalwa dan ma ana dankwafar da ita,karfe 9:30 daidai ta gama mika mai tayi ya amsa yana murmushi dana kasa gane maanarna sa

fitowarta kenan daga cikin aji,a gajiye take matuka ga kuma yunwar da take ji ita ta kara galabaitar da ita don tun safe har yanzu ko ruwa bata shaba"karon da sukayi ne ya dawo da ita daga duniyar tunanin data lula dago dara daran idanuwanta tayi ta dora akan kyakkyawar fuskar sa“”kallonta yayi a kaikai ce kafin yace "ke"zo muje bai jiran me zata ce yayi gaba abin"hmm kawai tace kafin tabi bayanshi,can bayan ajinsu suka tsaya dama tasan nan zasuje domin duk time din break shi yake sai mata abinci tun tana nauyin ci a gabanshi har ta saba,zai zauna ya jirata har ta gama amma fa ba maganar da zata hada su,ita har mamakinsa take yi amma kuma idan wani ya taba ta to fa anan ne zai nuna rashin mutuncinsa mutane abin na basu na basu mamaki yanda suka ga ammar na damuwa da duk wani lamari na jidda, domin kuwa ammar bai ragawa kowa a unguwarsu inba jidda ba"mtsww" tsakin da ya jane yasa ta dawo hankalinta kallon shi kawai tayi shiko ya tamke fuskar sa"idan ba zaki ci bane yasin zan zubar dashi"da sauri ta fara cin abincin,yanda take cin abincin ya sashi murmushi wanda ni kaina sai dana yi mamakin hakan“”tana gamawa kuwa ana komawa aji kowa ya shige ajinshi sai da yaga shigewarta sannan ya wuce shima

yana shiga ya nemi guri ya zauna "yadai my man auwal ne ya zauna a kusa dashi duk makarantar shi kadai yake kulawa saboda halinsu yazo daya,daga ina kake ne uhm ko dayake nasan daga gurin jiddah kake"uhm kawai yace danshi tunanin yanda zai ci uwar inna asabe da ya'ya'nta yake shegu masu kama da birai yace a fili,da sauri auwal ya kalleshi dan yansan mutane biyu ammar ya tsana duk duniya daga inna asabe sai umma matar babanshi dukan kafadanshi auwal yayi haba man ka share mutanennan mana haka ka bari mu hadu musu target kawai,sai yanzu yayi murmushi kafin yace ai qur'ani sai na cirema asabe awazu ita da shegun yaran nan' eh naji yanzu dai tashi mu haure ta gatanga kawai kasan fa yau madrid na wasa ko ka mantane"ban manta ba muje kawai to amma wa zai raka jiddah gida🤔 dallah muje zamu dawo kafin lokacin ok kawai yace tare da mikewa suka tafi

karfe 1:30 aka tashi a fitowa tayi ta tsaya a kofar ajin su ammar amma har suka gama fitowa bata ganshi
"ke"taji ance daga bayanta juyawa tayi suna fuskantar juna"waike wace irin mayya ce ne meye hadinki da ammar duk kin bi kin makale masa“”aysha kenan wadda aka fi sani da easha tana matukar son ammar amma shi bai ma san tanayi ba easha tana kyau daidai gwargado kuma babanta attajiri ne shiyyasa take abinda taga dama a makarantar tun farkon shigowarta ta ga ammar da suna dan mutunci amma tunda tace tana sonsa shike nan ya dauke mata wuta tare bata zazzafan kashedi wannan dalilin ne yasa ta tsani jiddah matuka take kuma mata wulankaci son ranta don ma ammar din yana taka mata burki ,sai data gama jirarta sannan taja yan korenta suka wuce, ita dai jiddah kanta na sunkuye dan ba iya fada tayi ba koma ta iya din ina zata kai easha ita dake kusan 18yrs kada kai kawai tayi ta fita a makarantar a kafa zata koma gida shiyyasa take ta sauri kar tayi lattin zuwa gida ta hadu da sharrin inna asabe"duk da yanzu din ma tana san ba tsira tayi ba

tun daga nesa tage hango wata dalleliyar mota a kofar gidan su ita dai a iya sanin duk danginsu bame ko mashin balle mota tunanin tane ya tsake saboda wadda taga ni ta fito daga motar RABI ce kanwar indo diyar inna asabe ta biyu sai famam washe baki take yi shiko na motar sai riko hannunta yake yi allah ya shirya kawai tace ta shige zauren gidansu turus ta tsaya ganin inna asabe na leke ta dan sakalen kofar batason da mutum a tsaye ba duhun data gani yasa ta dagowa da sauri cikin hargowar data saba ta fara magana don ubanki matsa in kalli abin arziki shegiya matsiyaciya tana bukulun kallon abin duniya yar bakin ciki kawai wuce ki bari wuri sum sum ta wuce cikin gida tana mai tirr da halin inna asabe

ur's Princes Deejerh💝
[16/01, 18:47] khadija ahmad dija Marubuciya Barauniya ce Frien Din Hassn: ✨✨BA DON SHIBA✨✨

By Princess Deejerh
New Writer

Dx Page is Dedicated To U Ramlat armanga (Real me dambu ce) ina godiya game da tunatarwarki a gareni ina yinki irin sosai dinnan😘💝

Page 1️⃣1️⃣ to 1️⃣5️⃣

kai tsaye cikin daki ta wuce tana mai kara yin tirr da halin inna asabe,,uniform kawai ta cire taji ana kwalla mata kira daga cikin gidan.da sauri ta fita tana amsa kiran''haladu ne tsaye rike da tulin kayan wanki a hannun sa watso mata su yayi tare da cewa 'ke' ga kayana na nan ki wanke min su yanzu nan,bai saurari me ba zata ce ya kada kai zai kara gaba,da sauri tace mai ina sabulun da zanyi wankin,kallon banza yayi mata kafin yace'' ina kudin da yake biyanki na iskancin da kukeyi ko ance miki bamu sani ba to ki cira a ciki ki siyo harara ya wurga mata da jan idon shi kafin yasa kai ya fice a gidan yana wani dage kafada waishi ga gaye,,kwasar kayan tayi ta nufi bakin rijiya kafin ta tashi shiga daki ta dakko ragowar sabulun data ajiye idan zata wanke kayanta

har ta fara wankin sai ga inna asabe ta shigo kamar an korota sai washe baki take daga bayanta rabi ce rike da manyan ledoji a hannunta''sai wani yatsinar fuska take,inna asabe kuwa jikina na rawa ta dakko bukiti ta juye ruwan zafi a ciki sai data surka sannan tayi hanyar bandaki ta kai''rabi fito ga ruwan can na kai miki kidan watsa ko kya ji dadin jikinki,daga cikin dakin ta fito rike da ledojin da ta shigo da su ke ta ce ma jidda a tsawace,da sauri jiddah ta taso ta bar wankin a bakin rijiya ''gani''tace a hankali, cikin yatsina ta fara magana kamar ansata dole ki dauki kayan nan ki gyara su duka kawai tace ta nufi hanyar bandakin,ba bata lokaci ta dauka ta fara dubawa ledar farko kajine a ciki dakwala har guda 6 dayar kayan miya ne a a ciki a da kayan dandano biyun kuma da suke gefe duk kayan fruit ne a cikin''kajin ta fara gyarawa sannan ta hura ice dakyar wutar ta kama,sannan ta dora akah,kayan miya ta dakko ta wanke ta zuba a karamin bokiti''nufar inda inna asabe take a zaune tayi ragwajab kamar kayan wanki sai faman faman washe baki take yau yarta tayi kasuwa,inna kudin nika kayan miyan yana da yawa''a hasale ta dago tace dan uwarki baza a bada ba da hannunki zaki nika shi in baki kudin nika ai kinji dadi kenan kin huta niko bana kaunar in ga kina hutawa nafiso kullum ingan ki a wahale jiya iya yau kamar yadda shegiar uwarki tayi har tabar duniya,wuce ki bani guri mai kama da zabaya yarinya sai bakin jinin tsiya.juyawa tayi ta tana share hawayen bakin ciki ,mahaifiyarta na kasa amma duk da haka bata tsira ba amma akwai allah,daukan kayan miyan tayi ta nufi inda ake ajiye turmi ta fara dakawa,,,

hajia umma ce hakimce a kayatacce falonta""gefen wata matace wadda kallo daya zaka mata kasan cikakkiyar yar duniya,duk da ita umman ta dan taba kafin ta samu alhj mu'azzam,hajia umma ce ta fara magana cike da takaici magajiya na rasa inda zan tsoma raina yaron nan ya gagareni baya shakkata ballantana tsorona na rasa ina zansa raina''rufe bakinta keda wuya magajiya ta antayo ashar tare da cewa kin bani kunya umma yanzu akan wannan dan yaron zaki tsaya kina tada hankalinki"katseta umma tayi da sauri'' tana fadin ke ammar fa da kika

ganshi ko ubanshi baya shakka ballantana ni amma in yasan wata bai wata ba ba'a ja dani a zauna lafiya“”yanzu naji zance kawata kawai kisan yanda zakiyi yabar gidan nan koma kasar gaba daya,da sauri hajia umma  tace kai kawata amma fa kin kawo shawara me kyau,wani killer smile tayi kafin tace ammar dani kake magana.

tafiya yake yana wani karkacewa ya zura duka hannu a aljihun wandon sa a bayansa kuma karnuka guda uku ke binsa duk inda yasa kafa kamar rakumi da a kala,duk inda yazo giftawa kafin ya karaso za ka ana darewa kowa yayi takansa,da sun san mistake kadan ne zai hadaku yanzun nan zai gwada ma rashin imani,isarsa kofar gidan yayi daidai da fitowar umma ta rako magajiya kofar gida.wucewa zatayi yasha gabanta sai data tsorata danganin fuskar sa ba alamun fara'a,cikin gadara ya fara magana ke tsohuwa bakiji jan kunnen da na miki ba ko wai gidan tsoho ne,da zaki damu mutane da zirga zirga to yasin na kara ganin ki wadan nan ya nuna karnukan sa su  rakaki har gida ko kuma insa addar nan in cire miki rabin kai,kallon addar dake hannun shi magajiya tayi tare da zaro,cikin rawar tace aa basai takai mu ga haka nama daina wallahi wuce shi da sauri tayi ko waige bata kara yiba,umma dake tsaye rai a bace ta bude baki zata fara surfa balaki kallon daya mata yasata fasawa tare da shigewa gida tana mai kara tsanar sa a ranta“”wucewa cikin gida yayi dan shi dama bacci ya kawoshi gidan

sai kusan laasar jidda ta gama ayyukan da inna da rabi suka sata,buta da dauka tayi alwala sannan ta shige daki ta fara sallah taji shigowa hadaladu sallah take amma sai da gabanta ya fadi dan kuwa kayanshi na nan bata wanke ba saboda aikin daya mata yawa.

Ur's princes deejerh💝
[16/01, 18:47] khadija ahmad dija Marubuciya Barauniya ce Frien Din Hassn: ✨✨BA DON SHIBA✨✨

By Princess Deejerh
New Writer

I dedicated dx page for u Hassan atk tanko Tnx for ur luv and support

Page1️⃣6️⃣to2️⃣0️⃣

cigaba da sallan ta tayi amma gabadaya rabin hankalinta yana kofar daki inda haladu ke tsaye yana ta surfo ruwan ashariya,kiran da ya kwalo mata ne yasa ta kara firgita amma fa duk haka bata katse sallan ba.cizge labulen bakin kofar yayi yana fadin ina wannan shegiyar tayi... cak ya tsaya ganinta tsaye tana sallah,kan uban can yace da karfi wanda yayi sanadiyyar fitowar inna asabe daga cikin daki..dan dama tana jinsa kyaleshi kawai tayi ya gama na shi kafin ta dora nata,shiga cikin dakin yayi tare da fincikota ya wurgo ta waje kamar kayan wanki,,ita dai jiddah

baiwar allah ba bakin magana dan tasan yau allah ne kawai zai iya ceton ta a hannun azzalumi haladu..shigowar indo da talatu ya katseshi tare da cewa yauwa kunzo a daidai kuzo ku cimin uban wannan zabayar,,shewa suka sa a tare dan dama su kamar jira suke,,hakuri jiddah ta fara bashi tare da fadin kayi hakuri inna ce ta sani ayki....ai bata karasa ba asabe ta kai mata naushi a baki tana fadin"kujimin yar iska zata min sharri yaushe na saki aiki ina ce hijabi kika zara kika tafi gun wannan tantirin yaron,yau saikinci ubanki a gidannan..dukan su suka rufu akanta suna dukanta kamar sun samu jaka da kansu suka gaji suka kyaleta,,ita kuwa jiddah baiwar allah a wannan lokacin bata da bakin magana domin bakinta yayi suntum jikin duk ya farfashe sai sheshshekar kukan ta ke tashi,,daga inda take tana jiyo shewar su a can kuryar dakin inna asabe.suna yi suna cin naman da tasha wahala gun dafa shi"da kyar ta samu ta rarrafa ta shige cikin daki akan katifar ta kwanta wadda bata da maraba tsumman gogegoge ta kwanta,,kafin kace me zazzabi ya rufeta dakyar ta jawo hijabinta ta lullube tana mai kara tausayin rayuwarta,,

a bangaren ammar kuwa baccin shi yake cikin kwanciyar hankali kiran sallah la'asar ne ya farkar dashi daga baccin da yake,domin kuwa duk iya shegen ammar baya barin sallah ta wuce shi gashi da tausayi.amma fa idan ka shiga gonar shi to fa ba mutunci

sai da ya idar sallah sannan yayi cikin gidah umma ce hakimce a falo tana kallon tv tana jefa fruit  a bakinta,,wucewa yazo yi ta gabanta ko kallon inda take bai yiba,,babanka na hanya gobe,, juyowa kawai yayi ya kalleta kafin ya wuce..da harara ta bishi kafin tayi kwata ka kusa kama gabanka ai,,shidai baima samd tanayi ba..kicin ya shiga ya dakko abincin sa ya fice daga sashen gaba daya,,,yana gama cin abinci ya shiga wanka be dade ba ya fito shiryawa yayi cikin wasu riga da wando rigar me dogon hannu ce wandon kuwa jeans ne amma duk amma sa crazy,wata sarka ya jawo me uban nauyi ya dora ta a wuyanshi..sannan yasa pcap a kanshi,,ya fito a dan dabanshi sak amma hakan bai hanashi yin kyau ba..ficewa yayi a gidan a 360,,,

kiran sallah magribtne yasa ta mikewa dakyar ta rarrafa ta dauki buta alwala tayh kafin ta kara komawa cikin dakin dakyar ta samu tayi sallan ta kara komawa ta kwanta dan har yanzu zazzabin bai sake ta,,tana jiyo hayaniyar inna asabe da yayanta dan dama su sallah ba damun su tayi ba ,,kwala mata kira taji anayi kuma muryar inna asabe ce..cire lullubin tayi ta maida tasa a jikinta sannan ta nufi kofar dakin,,sallama tayi ba wanda ya amsa a cikinsu.sai wurgo mata kudi  indo tayi tana fadin wuce ki siyomin pad a shagon sile bana son na shagon rabe,toh kawai tace tare da amsar kudin tayi hanyar waje,tafiya take kamar zata fadi amma haka ta cigaba,,

fitowar shi kenae daga masallacin su uku ne ammar auwal da kuma nura,tafiya suke da sauri domin time din wasansu ya fara,,tun daga nesa yake hangota tana tahowa a yanayin daya ganta yasa fuskar shi sauyawa,ina zuwa yace ma su auwal kafin ya isa inda take kallonta yake tun daga sama har kasa,dagowa tayi tana murmushin dole wanda yafi kuka ciwo,,waya miki haka kawai ya ce dan sai data dago kanta sannan yaga bakin ta a fashe ga kuma idonta daya kumbura,,kan uban can yace da karfi tare da zaro mata idanu,, tambayarki fa nakeyi yace a

hasale,,a hankali ta fara fada mai abinda ya faru tare da fashewa da kuka,,,,,kutumar uba yau sai naci uban uban asabe sai na karya wa haladu kafa,,kai yau duk wani daya shafh asabe sai mun mai operation huci kawai yakeyi a lokacin da zai ga su haladu ba abinda zai hana bai cire ma tsohuwar nan da yayanta kafafuwa ba,,,maganar dayake da karfi ne ya janyo hankalinsu su auwal dama sun tsaya saboda karsu damesu,,, auwal yace yadai my man dogon tsaki yaja kafin ya basu Ibrn abinda ya fara,,,,yeeeehuuuu,,cewar auwal kace yau anta bomu tunda aka taba jidda kai nura jeka tattaro su duna da bahago dukakasu da sauri nura yayi hanyar barin wajen domin cika aiki,,kara kallonta ammar kafin jeki gidan maman sahala zanzo in sameki,,,,

Toooh yaufa su inna asabe an taro pillars

yawan comment yawan typing

Ur's princess deejerh💝
[16/01, 18:47] khadija ahmad dija Marubuciya Barauniya ce Frien Din Hassn: ✨✨BA DON SHIBA✨✨

By Princess Deejerh
New Writer

wannan shafin sadaukarwa ne gareku daukacin members na zahra surbajo novel facebuk commen dinku namin dadi I HEART U ALL😘😘

Page2️⃣1️⃣
to2️⃣5️⃣

Sai daya ga ta shige gidan maman salaha sannan ya juyo ya fara tafiya yana saka irin rashin mutuncin da zaiwa haladu da uwarsa,,a bakin layin ya hadu dasu auwal ni kaina sai dana tsorata😳ganin irin mutanen dake tare dashi,gaba dayansu ba alamun murmushi a fuskar su jira kawai suke ace kule suce cass...duna ne ya fara magana yana ciccezewa..yadai baba wai aina za ayi operation din ne kasanfa kwana2 ban fede ba,,murmushin mugunta ammar yayi kafin yace ku biyoni muje..duuu kuwa suka bi bayanshi kusan su 15 ne amma duk shine a gaba kowane da makami kuma a hannun sa tun daga nesa da an hango su zaa fara gudu..dan mutane sunsan ba alheri bane ke tafe dasu ba,,wasu daga cikin mutanen kuwa har sun tausayama wanda zasu je gurin shi..domin kuwa ba yau aka saba ganin haka ba sai dai kowa

yayi gumm ba bakin magana,,

jidda zaune a acikin dakin maman salaha amma hankalinta gaba daya baya jikinta tana tsoron abinda ammar zaije yayi...da karfi maman salaha ta kira sunanta sannan ta dago a firgece,,ke kuwa jiddah me yayi zafi haka,,cikin kuka ta labarta mata halin da ake ciki,,allah na gode maka maman salaha ta fada tare da kwashewa da dariya..tabbas ammar ya cika dan halak kuma yamin daidai,,da sauri jidda tace amma fa kada su mai wani abu daga baya,,hmm tace kafin ta fara magana jiddah kenan kinsan uban ammar nada kudi ba abinda zasu iya yimai,,sai da ta kwantar mata da hankali kafin taje taci gaba da aykinta

zirga zirga kawai suke a cikin gidan daga ita sai haladu domin su rabi tuni suka fice yawon su amma fa indo ta kullaci jiddah a ranta tun dazu ta aiketa amma bata dawo ba..da tunanin rashin mutuncin da zata mata inta dawo ta fita aranta,,,,,kofar gidan sukaji ana bugawa..da karfi kamar zaa cire inna dake tace kamu ta duro ashar kafin tace wani matsiyacin ne zai ballamin kofa shegu yan bakin cikin unguwa zasuja min asara,,shiko haladu da fitowar sa kenan daga bandakin ya fara zubo nashi ruwan ashariyar dan kuwa karan buga kofar ne yasa shi fitowa ba shiri,,,daga can waje kuwa ammar ne da gang dinsa tsaye mamakin zagin da tsohuwar da danta ne sukeyi ya kamasu duk da shi ammar yasan zasu iya fiye da haka,,,cikin fushi yama kofar zuwa daya sai gata a gefe.shiyya fara shiga cikin gidan sannan sauran suka biyo bayanshi..mute bakin inna asabe yayi ganin ammar da yan jagaliyanshi sai da kirjinta ya buga domin kuwa bata manta warning din daya mata kwanaki ba...shiko haladu me danyen kai zaburowa yayi wai zai naushi ammar zuwa daya ya kamashi hannun ya murda.ihun azaba haladu yasa naushin bakinsa yayi tare da jefar dashi a kasa gwajab kamar kayan wanki,,cikin daga murya ammar yace dasu operation start...aiko basu yi wata wata ba suka fara fasa duk wata roba ko bokiti dake tsakar gidan wasu kuma dakuna suka shiga suka fara tarwatsa kayan tsummokaran data tara kai hatta igiyar shanya  basu barta ba,,,tukwanen kuwa sai da duk suka taka su duk suka lauye,,nuna musu haladu yayi dake kwance har yanzu yana jinyar hannun sa,,ku kawo min shi nan dakko shi suka yi suka ajeyi a gabanshi baiyi wata wata ba ya kai mai naushi a fuska sai ga jini nabin gefen fuskarsa,,inna asabe na ganin haka tasa ihu tana neman agajin makota,,,jama'a ku kawo mana dauki ku taimako ga jujal nan da mukarraban sa...naushin da duna ya kai matane ya sata rufe baki bata shirya ba ai ko jini ya fara malala  mangareta duna yayi ta fadi kafin su rufe su da dukansu bame ceton wani

Ur's princes deejerh💝
[16/01, 18:47] khadija ahmad dija Marubuciya Barauniya ce Frien Din Hassn: ✨✨BA DON SHIBA✨✨

By Princess Deejerh

New Writer

Page 26 to 30

Sai da ammar da yaransa suka musu wulakanci na bugawa a jarida shafin farko,,,sannan yasa suka kara buge haladu.,inna asabe kuwa tunda aka mata zuwa daya har yau tana kwance shame shame rike da kafarta da wani ya taka mata a cikinsu,,,sai da suka gama duk wulakancin da zasu musu sannan suka fice suka barsu kwance anan bamai taimakon wani a cikinsu,,

fitowar su yayi daidai da komawar kowa cikin gidanshi...dan dama duk mutane najin abinda ke faruwa

sai da jidda taci abinci tayi sallai ishai sannan taiwa maman salaha sai da safe ta tawo gida,,,tana zuwa kofar gidansu gabanta ya fadi ganin kofar a yashe a kasa tasan wannan aykin ammarne..da sallama ta shiga gidan,,su rabi ta samu zaune kusa da inna asabe tana gasa mata kafa da ruwan zafi ita kuma asiya da indo suna kan haladu suna goge mai jinin da ya bata mai fuska duk fuskar nan ta kumbura sai ya kara muni kamar irin horror dinnan....kowa ido ya bita dashi ba halin magana domin su rabi sunji labarin abinda ya faru shiyyasa ba wanda ya tanka mata..daki ta shige kawai tayi kwaanciyar ta..

Tofa tun daga wannan ranar baima dukan jiddah a cikinsu sai dai abita da harara da kuma tsaki..aikin gida ne dai haryau ba fashi,,

Haka rayuwa ta cigaba da tafiya duk da gidan ba dadi amma yafi da tunda yanzu har abinci ana bata kuma bata musu wanki saidai girki da gyaran gida,,a bangaren ammar kuwa har yanzu umma tana nan tana hada mai tarko duk da abbansa baya yadda,,amma dai bata karaya ba tayi alkawarin sai ya bar gidan duk daren dadewa,

A yanzu jiddah tayi jss c.e kuma ammar ne ya mata komai duk shima wannan shekarar zaigama scondry skul,,da kansa ya mata registration anan makaran tarsu aka bata ss1 science class,,tana makaranta cikin kwanciyar hankali da wuri take tashi ta gama duk ayyukanta na gida sannan ta shirya ta tafi,,tana fitowa zata samu ammar a bakin layi shi zai rakata har bakin makaranta sannan ya bata kudin break,tunda yabar makarantar haka yake mata duk da shima abbansa na neman masa makaranta,,,

inna asabe ce zaune ita da lami,,lami kawar inna asabe ce tun yarinta dan wasu halayen duk ita

ta koya mata dan lami bata zaman aure ga bin bokaye,,inna asabe ce ke bata labarin abinda ammar ya musu har gida,,,mtsww lami taja tsaki kina aikin me har haka ta faru idan hagu takiya ai sai a koma dama,,tun farko sai da nace miki mukai sunanta gurin na bakin rafi amma kika ki to yanzu wa gari ya waya ke mana,,duk layi anata yi dake yayanki sun lalace ita kuma sai yabonta ake,,wannan yabon shi zamusa ya koma aibatawa,,yanda shikansa ammar din sai ya kyamace ta,,tabbas kawata kin kawo shawara me kyau gobe da sassafe zan shirya in biyo ta gidanki sai muje gurinshi,,yauwa ko kefa ki maidata abin kwatance,,ki dauki fansar abinda ammar ya miki dan na tabbatar sai yafi kowa shiga kunci idan ya ganta ,,,ai fa nagode lami nida duk banyi wannan tunananin ba,,,har kofar gida ta rakota suna kara tattaunawa akan muguntar da zasu ma baiwar allah da bata rikesu a zuciya ba...

Da daddare jiddah na zaune kofar daki itama inna asabe suna zaune ita da yayanta firar su suke cikin kwanciyar hankali,,sai dai kawai taji suna shewa,,kadaici ne duk ya isheta ina ma tana da iyaye da rayuwar ta bazata zama haka,,wani yaro karami ne ya shigo gidan,yace ana kiran jiddah a waje,,ba wanda ya tanka a cikinsu itace tace kace gani nan zuwa dan tasan ammar ne,,hijab kawai tasa tafita a tsaye ta same shi a kofar gidan,,gaeshe shi tayi ya amsa cike da kulawa,,shiru ne ya biyo baya kafin ya fara magana cikin sanyin murya kamar ba ammar ba,,,jiddah ya kira sunanta da sauri ta dago ta kalleshi domin kuwa yanda ya kira sunan nata ne ya sanyaya mata jiki,,ce mata yayi ga wannan amsa kawai tayi ba tareda ta duba ko meye ba,,shine yace atm carda dina ne sannan ga waya nan itama ya miko mata..amsa kawai tayi tana jiran karin bayani,,,jiddah zanyi tafiya mai tsawo abbana ya sama min makaranta a noida university india,,da sauri ta dago ta kalleshi domin kuwa maganar ta bugeta tuni har ta fara hawaye,,shima dakewa kawai yakeyi amma da ba abinda zai hana shi yin kuka amma bayaso ya karya mata zuciya,,,kuka ta fashe dashi da karfi domin ji take in ammar ya tafi kamar wani abu zai faru,kiyi hakuri jiddah ai zan rinka zuwa hutu akai akai,,,ita dai bata saurare shi ba kukanta kawai takey..jin kukan yake har cikin ransa,,,shima dan dai ba yadda zeyi ne abbansa ya matsa masa amma da ba wanda ya isa yasa shi zuwa wata kasa karatu,,dakyar ya samu ya lallabata har tayi shiru amma fa a zuciyarta ji take kamar ta mutu saboda bakin cikin tafiyar ammar,,,da kyar ya lallaba ta har ta shige gida,,shima ya tafi

a wannan daren ba wanda ya runtsa a cikinsu ,,,dan jiddah kwana tayi tana kuka...shi kuwa tinana shi wani hali zata shiga bayan tafiyar shi...

Ur's Princess Deejerh💝
[16/01, 18:47] khadija ahmad dija Marubuciya Barauniya ce Frien Din Hassn: ✨✨BA DON SHIBA✨✨

By Princess Deejerh
New Writer

Page 31 to 35

Haka jiddah ta raya wannan dare tana kuka..da ta tashi da safe kuwa fuskar nan tayi jajirr abinka ga farar mace,,idanuwan nan sunyi luhu luhu..a sanyaye take komai dan har yanzu zuciyarta bata dena mata zafi na tafiyar ammar ba...

Zaune yake a gaban abban shi fuskar nan a daure..sai ya dawo sak ammar din dana sani mara son wasa,,domin kuwa yayi tinanin abban shi zai goya mishi baya daya ce baya son tafiyar,,,abban ne ya fara magana cike da fushi...ammar kenan kai bakaji kunyar tunkara ta da wannan maganar ba kalleka fa shekara 22 sai yanzu ka gama scondry skul sa'annin ka duk tun yaushe suka gama saboda kai bakason cigaba kome?to wannan karon babu fashi gobe jirgin ku zai tashi da yamma ka gama duk wani shirinka dole ka tafi,,kai kafi so ka zaunj a gari kana yawo da abokan banza ana maka gata amma kai baka gani baza ka gane gata ake maka ba tukun sai nan gaba idan kayi hankali,,,tafiya kam ba gudu ba ja da baya na gama maka komai...ka tashi kaje ka cigaba da shiri,,,tun da ya fara fadan kanshi na sunkuye amma fa ji yake kamar zuciyar shi zata fashe saboda takaicin tafiyar shi,,,tashi suka yi duka kowa yayi dakin shi,,,da sauri umma dake labe tana jin duk yanda suka yi itama ta shige dakinta,,,waya ta dauka ta kira laraba ringing biyu ta dauka cikin farin ciki umma ta fara fesa mata duk halin da ake ciki,,dariya itama kwashe dashi sannan tace, ai na fada miki idan har kika yi haka dole yabar gidan tunda abbansa yana son yaga yayi karatu kafin nan da 5yrs din ai mun gama abinda zamuyi mun kara gaba,,,aikuwa dai laraba akwai ki da basira,,,kin mantani kenan umma wai dan ma nayi sanyi kenan,,,,to shknn jibi kizo da sassafe akwai magana tunda shi abban nasa ba zama zaiyiba,,,to shikenan...

Inna asabe da lami zaune a gaban na bakin rafi..lami ce zata fara fada mashi abinda ke tafe dasu,,,da sauri bokan yace mun riga mun sani tun shigowar ku dajin nan,,,yar mijinki ke baki matsala me kike so a mata a haukata ta ko a kashe ta,,,da sauri lami tace aa boka so mike a lalata rayuwarta ta koma kaman karya yanda al'umma zasu kyamace ta ta koma abin kyama,,,,katseta bokan yayi tare fadin ba yanzu ba,,,domin kuwa yanzu ba aljanin da zai iya zuwa ya rabeta dan tana ibada kuma ko yaushe cikin karatun qur'ani take duk aljanin da yaje kusa da ita kuwa yanzu to lalle sai ya kone,,,,inna asabe ji tayi kamar ta kurma ihu dan takaici taga samu taga rashi,,da sauri tace to yanzu boka ya zamu yi,,,,,cikin daga murya yace zan baki wani magani kullum ki zuba mata a cikin abinci indai tana ci to a hankali zata fara daina ibada zai saka mata kasala to a wannan lokacin ne zamu aiwatar da shirin mu a kanta,,,,amsa lami tayi tare da fadin mun gode boka,,kudi inna asabe ta ciro ta ajiyemai a gabanshi,,sannan suka fita....tafiya ce me nisa sosai tsakanin gurin da bakin titi,,inna asabe ke cewa lami,,to yaya zan bata maganin tunda kullum ne,,,mtsw lami taja tsaki kafin tace ta inda aka hau ai tanan ake sauka...nuna mata zakiyi komai ya wuce ta yafe miki ke inta kama har kuka kiyi ta yanda zata

yarda kinyi nadama to ke kuma kinga kin samu hanyar yi mata komai tunda zata yarda dake,,,,tabbas shawarar ki tayi lami muje gidan dae....

atm card din daya bata ne a hannun ta ga kuma wayar a gefe..duk wannan basu take bukata ba tafi bukatar shi a kansu lokaci daya haka kwatsam...kuka ta kara fashewa da shi tana mai fadin allah ka kawomin dauki a rayuwata,,sallamar inna asabe ce ta katse mata kukan da takeyi...abin ya bata mamaki inna asabe da sallama bata kara jin mamaki ba sai da taga inna asabe ta leko tana fadin sannu jiddah ya gida,,da sauri ta mike ta fito waje dan kuwa har yanzu bata gama gyara gidan ba,,,kuma tana kara mamakin inna asabe,,zo nan jiddah taji ance daga bayanta cikin tattausan lafazi,,juyawa tayi ta nufi kofar dakin indainna take a tsaye,,,jiddah"da sauri ta dago kanta ido ta zare ganin inna asabe ido jajirr da alamu tasha kuka,,cikin muryar kuka ta fara magana jiddah ki yafemin na zalunce ki na cuceki tun kina karamar ki,zubewa tayi bisa gwiwarta tana mai kara fadin ki hakuri jiddah ki yafemin ko zanji salama a raina ina cikin kunci kada in mutu da hakkin ki a kaina ki yafemin dan allah jiddah tare da fashewa da kuka mai ban tausayi,,,,da sauri jiddah ta dago ta tana fadin inna kefah uwata ce bai kamata ki tsugunna a gabana ba wallahi na yafe miki,,,ngd jiddah cewar inna asabe allah ya miki albarka yata ta kaina,,bakomai inna komai ya wuce,,to jiddah jeki kwanta ki huta kema zatayi musu inna asabe tace lallaifa saidai ta kwanta,,ba yanda zatayi ta juya ta shige dakinta tana mamakin abinda ya faru ayau,,,inna asabe kuwa dariyar mugunta tayi kafinta tace yaro bai san wuta ba sai ya taka.....

yanzu aka fara

masoya novel dina kuyi hakuri da jina shiri kwana2 hakan ya faru ne saboda wasu dalilai amma yanzu zaku rinka ganin shi akai akai kamar yadda muka fara

Ur's princes deejerh💝
[16/01, 18:47] khadija ahmad dija Marubuciya Barauniya ce Frien Din Hassn: ✨✨BA DON SHIBA✨✨

By Princes Deejerh
New Writer

wannan shafin sadaukarwa ne ga ku masoya novel dina ina jin dadin yadda kuke bibiyar novel dina da kuma numa min kaunar da kukeyi,nima ina kaunar ku irin totallay dinnan😍😍

Masu cewa a kara yawan page kuma bana typing kullum kuyi hakuri ayyuka ne suka shamin kai amma insha allah very soon zaku fara jina kullum luv u oll😘

Page 36 to 40

Haka washegari ma data tashi abin mamaki baya karewa,,inna asabe da su rabi ne wai ke aikin gida😨karasa wa tayi gurin da suke kafin tace inna kawo wanke wanken in miki,,,da sauri inna asabe tace haba jiddah ai yanzu lokacin hutunki ne ki bari kawai muyi kinji yata ga abincin ki can a dakina ki dauka kije kici sai ki koma bacciin ki,,har ta bude baki zata yi magana inna asabe ta kara katseta haba jiddah baki daukeni uwa bane kome,,aa inna ba haka bane..to kiyi abinda nace kinji jiddah ta,,,juyawa tayi taje ta dakko abincin cikin dakin su ta shige ta zauna tana godema allah daya sa inna da yayanta suka gane gaskiya,,cikin kwanciyar hankali take cin abincin can kasar zuciyar ta kuma tunanin ammar ne fal cikinta..

sai da inna asabe taga shigewarta daki sannan taja tsaki,,rabi ce ta fara cewa,,gaskiya inna jiddah wawiya ce wallahi lokaci daya muka sauya mata kuma wai harta yadda dan shashanci,,hmm kedai bari yarnan ji nake kamar in shaketa amma inaa sai lokacin da burina ya cika sannan zanyi bacci me dadi ina so inga jiddah ta wulakanta ta zama abar kwatance ta yanda ita  kanta sai ta tsani rayuwar ta(nikam nace ta allah ba taki ba jiddah tafi karfinki eheee😡😡)

tunda da dare ammar ke tunanin halin da zai bar jiddah,,ya rasa gane me yake ji akan ta soyayya ko kuma tausayinta kawai yake,,maganar auwal ne ta fado masa a rai..a koda yaushe maganar shi kenan son jiddah kake matuka amma ka kasa ganewa koda yake watarana zaka gane,,hmm ajiyar zuciya ya sauke a hankali daya tuno inna asabe dole ne yakama mata warning kafin ya tafi da wannan tunanin bacci ya daukeshi...

tana gama cin abincin ta fara shirin skul fitowa tayi dan tafiya har takai bakin gida taji inna asabe na kwala mata kira,,juyawa tayi ta koma ciki,tsaye ta ganta a bakin daki,,kudi ta miko mata naira 100 gashi kyasai wani abu ko,,amsa tayi tana godiya kafin ta juya ta tafi,,,tana isa bakin layin ta tarad da shi tsaye,,shima yana ganinta ya taso ya karaso inda take,,gaeshe shi tayi a ladabce..bai amsa ba sai ma kura mata ido da yayi,,dan yaga alamun kamar tayi kuka,,tambayar yayi meya faru,,murmushin yake kawai tayi sannan tace bakomai..jinta kawai yayi amma yasan akwai abinda ke damunta,,kodai asabe ce,,da sauri ta dago ta kalleshi kafin tace ai inna ta sauya yanzu tana sona ta fada tana murmushi..me kika ce ya fada da sauri,,abinda ya faru duk ta fada mishi..shidai yaji kawai amma fa bai yadda da canzawar asabe ba,,akwai wata a kasa yace a hankali,shareta kawai yayi ya taran mata napep tahau,,tana wucewa shima ya wuce gida domin da yamma jirgin su zai tashi,,amma kuma zuciyar shi ta kasa yadda da asabe dan tabbas akwai wata a kasa amma kafin ya tafi sai yaje gidan tabbas...

karfe 1 jiddah ta dawo gida tana shiga daki ta samu abincinta a rufe sai da tayi sallah kafin ta ci

abincin..wayar da ammar ya bata ta dakko tana dubawa,,daga yau shikenan ba zata kara ganin shi ba har sai bayan 5yrs hawaye ne ya fara zuba a idonta kafin ta fashe da kuka,,lafiya jidda taji an fada daga baki kofa da sauri ta fara goge hawayen idonta ta fara kokarin kakalo murmushin dole,,karasowa tayi ta zauna kusa da ita kafin tace ki fadamin meke faruwa yanzu nice mahaifiyar ki jiddah kinji fadamin,, maganar tafiyar ammar ta fada mata,,ai inna asabe kamar an mata bushara da gidan aljannah haka taji,,amma da yake munafuka ce sai ta kwabe fuska alamun tausayi ayya jiddah ni kaina naji ba dadi amma wannan shine daidai kinga fa karatu zaije kawai ki masa addu'a da haka ta rinka kwantar mata da hankali har ta samu nutsuwa,,,har ta juya zata fita a dakin ta hango waya a gefen jiddah,,dawowa tayi ta dauki wayar wannan fa jiddah,,abinka ga yarinta sai cewa tayi ammar ne ya bani har da atm card dinsa ya bani,,kinga yanzu ki kawo in aje miki su idan ya tafi saiki fara amfani dasu ko jiddah ta,,washe baki tayi tace to inna asabe

inna asabe na komawa daki ta samu su rabi zaune dama jira suke ta dawo,,ya akayi ne inna indo tace,,kwashe duk yadda suyi da jiddah ta fada musu,,kai amma fa munji dadi aikin mu zai tafi yadda akeso kenan wannan dan daban bayanan,,inna asabe ce tace ke rabi zo in aikeku unguwan rimi keda jiddah kada ki dawo har sai na kiraki a waya dan bana san su hadu har ya tafi nima fita zanyii....

Ur's princes deejerh💝
[16/01, 18:47] khadija ahmad dija Marubuciya Barauniya ce Frien Din Hassn: ✨✨BA DON SHIBA✨✨

By Princess Deejerh
New Writer

Zuwa ga masoya BA DON SHIBA musamman wadanda suke min magana ta watsap da kuma Sms plss ku cigaba da yimin hakuri ina busy ne 2days amma amma INSHA ALLAH na kusa kammala komai zaku rinka ganin shi akai akai saboda haka wannan shafin sadaukarwa a gareku kuyi yadda kukesodash😘😘
💝💝luv u oll💝💝

Page4️⃣1️⃣ to4️⃣6️⃣

kafin kace me har rabi ta gama shiryawa sai a lokacin inna asabe taje ta fada wa jiddah maganar da aiken data musu,,bata kawo komai a ranta sai ma shiri data fara yi tana gama wa rabi tace su tafi..kudin mota inna asabe ta basu sannan tace suyi sauri su tafi,,suna fita mota suka hau suka wuce,,koda suka isa gidan sun tarar bata nan amma sai rabi tace su zauna su jirata kila ba dadewa zatayi ba ta fada kawai domin daga ita har innan sun san bata nan,,zaman

taga bana karewa bane gashi kuma ta fara tunanin tafiyar ammar har 4:30 a lokacin amma taga rabi bata da niyyar tashi su tafi,,so take ta mata magana tace su tafi amma ta kasa,,dakyar ta daure tace mu tafi gida mana tunda yamma tayi gashi kuma har yanzua bata dawo ba,,murmushi kawai rabin tayi kafin tace kiyi hakuri jiddah kinsan halin inna idan muka koma babu sakon nan mita zatai tayi,,,ita dai jiddah bata kara magana ba amma fa zuciyar ta fal ta cika da kunci kamar ta fashe da kuka haka take ji dan tasan 5:30 jirgin su ammar zai tashi allah yasa ma a fasa tafiyar(niko nace ai ba fashi jiddah)

karfe biyar dai dai ammar ya tsaya a kofar gidan su jiddah yaron da ya ayka cikin gidan ne yaga ya fito yana fadin wai batanan,,batanan ya maimaita cikin mamaki ina zataje yau friday a wannan lokacin...muryar inna asabe ce ta katseshi tana fadin ai jiddah bata nan sun fita da maman salaha ta rakata zaria kuma naji kamar suna cewa sai gobe zasu dawo...tunda ta fara magana ya bata rai taya zata fita bayan tasan yau zai tafi kuma yacea mata yau din zai zo suyi sallama,,bai ce mata komai ba kawai ya juya dan ranshi a matukar bace yace,,,tafiya kawai yake yana tunanin abinda jiddah tayi,,yana zuwa gida bai tsaya komai ba ya samu abban shi a bakin mota dama shi kadai yake jira dan sun gama komai ko kallon umma dake mai ALLAH ya kiyaye hanya baiyi ba shigewa kawai yayi ya zauna kafin shima abba ya shige ya tada motar,,umma ji take kamar an mata bushara da gidan aljannah yau ammar zai bar kasar sai kuma bayan 5yrs zai dawo,,,
tana ganin fitar su a gidan itama ta fice...

sai karfe shida jirgin su ya tashi ya tafi cike da kewar jiddah domin har hawaye sai da ammar yayi yana kuma jin haushin yanda bai hadu da ita ba,,

sai da sukayi sallar magrib amma har a lokacin bata dawo ba,,sai a lokacin inna asabe ta kira rabi tace su dawo,,shirin tafiya suka farayi,,amma jiddah jikinta a sanyaye tanaji a jikinta ammar ya tafi,,hawaye kawai takeyi a cikin mota amma ba wanda ya lura da hakan,,,suna karasa wa gida sallah ta farayin kafin a miko mata abincinta takai abincin baki kenan..taji inna asabe tace dazu kuwa ammar yazo miki sallama amma bakyanan shine yace to in fada miki ya wuce,,kasa kai abincin bakinta tayi sai hawaye daya fara zuba kamar an bude famfo fadawa daki tayi da gudu kuka takeyi kamar ranta zai fita shikenan ba zata kara ganin sa,,kuka ta kara fashewa dashi...inna asabe kuwa jin kukan take kamar sautin kida ba abinda takeso irin taga jiddah cikin kunci cikin masifa da bala'i amma da yake munafuka shiga dakin tayi ta fara lallashin ta har ta dan tsagaita,,haka jiddah ta kwana tana tunanin ammar tana kuma addu'ar allah ya kareshi duk inda yake,,(masoyin gaskiya kenan)

ammar mutanen india an sauka lafiya dama akwai abokin abba shine ya aiko a dauke shi isar su gidan keda wuya yaga kowa yana ta nan nan dashi daga shi sai matar sa da ya'ya'n su biyu duka maza dayan mai suna abbas sa'an ammar ne sai kuma karamin wanda baikai 20yrs ana ce masa annur,,yanda suka rinka tarairayar sa shi yasashi farin ciki sosai,,,sai daya yi kwana2 yana hutawa kafin ya fara shiga skul shida abbas,,,ammar ya maida hankali sosai a karatun shi

ba ruwan shi da babes din dake tururuwa akanshi bakake da fararen wasu abota suke yin dashi wasu kai tsaye zasu nuna sonshi baya kula su dan shi ba tasu yake ba mace daya keda wannan matsayin kuma baya tare da ita amma kullum da ita yake kwana yake tashi a ransa,,har su abbas sun san labarin jiddan ammar,,haka rayuwa take ta tafiya cikin kwanciyar hankali,,

a bangaren jiddah sai ince maganin inna asabe ya fara ci dan yanzu tana ji ana kiran sallah amma bata damu ta tashi tayi ba,bata karatun Qur'ani ballantana kuma azkar din da takeyi haka kawai zata rinka jin kasala a jikinta ko kuma jikinta ya mata nauyi,,inna asabe tana cikin farin ciki tana lura da duk halin da jiddah ke ciki har tana shirin komawa wajen boka ya cika mata aikin da suka fara....

Ur's princes deejerh💝
[16/01, 18:47] khadija ahmad dija Marubuciya Barauniya ce Frien Din Hassn: ✨✨BA DON SHIBA✨✨

By Princess Deejerh
New Writer

Alhamdulillah na gode da addu'ar ku gareni masoyana insha allah yanzu na dawo ba wani sauran jinkiri...
Luv u oll😘

Page 4️⃣6️⃣ to 5️⃣0️⃣

Jiddah rayuwa ta fara sauya mata domin kuwa maganin inna asabe ya fara tasiri a kanta a yanzu jiddah sallah bata dame ta ba,,makarantar ma yanzu tana SS2 amma ta daina zuwa bata karatun alqur'ani data saba yi duk safiya,ita kanta tana jin wani iri a jikinta amma kuma tana son yin karatun amma data fara sai taji kasala ta rufeta,,,

tabbas asiri gaskiyar mai shi wannan haka yake ta bangaren inna asabe da ya'ya'nta domin yanzu farin ciki suke ciki kamar an basu kyautar kujerar makkah,,,

a safiyar yau ne inna asabe ke shirin komawa wajen bokanta domin yin aiki na karshe a kan jiddah saboda haka tun asuba ta tashi tana sauri ta fita dan kar ta tarar da layi haka nan take jin farin ciki a cikin zuciyar ta..ko farkawa bata bari sunyi ba ta zari mayafi sai gidan boka...tana zuwa bata tarar da kowa ba dan ta bugo sakko...yana ganinta ya fara washe wagegen bakin shi wanda ba haure ko guda daya a ciki,,magana ya fara mata da katuwar muryar sa,,lallai ke jaruma ce muna son aiki da irin ku wadan da basa bata mana aiki,,,saboda haka wannan ma

aikin naki tabbas zan miki me zafi..wata laya ya ciro a kasan inda yake zaune tare da mika mata layar,,,tana rawar jiki ta amsa..wannan layar a kasan inda take kwanciya zaki haka rami ki binne ta,,sannan ya kara dakko wani garin magani ya mika mata,,wannan kuma ki zuba shi a daidai inda kika san zaka taka,,tofah da taka kuma ta kwanta akan wannae layar aikinki
ya gama,,,amma kuma da sharadi,,sharadin meye boka inna asabe ta fada,,dan kuwa ita a ranta ko meye sharadin zata yarda komi munin shi kuwa indai jiddah zata wulanka a idon duniya,,,sharadin kuwa shine duk randa aka tona wannan layar to wannamd asirin kan daya daga cikin ya'ya'n ki zai koma,,duk da ta tsorata amma hakan bae hana ta amsawa ba da ta amince,,dan kuwa tasa aranta bame tonewa,,
shidai boka maimaita mata yake yi,,amma da yake zuciyar ta ta kekyashe bata damu ba,,,kudi ta ciro ta mika masa sannan ta fito ta fara tafiya dan samun abin hawa,,,

Ammar ne zaune a compound din gidan shi kadaine amma kallo zaka masa kasan ya lula duniyar tunani ,,abbas ne tsaye akan shi amma shi baima sani ba,,,ruwan dake hannun sa ya yarfa masa,,firgigit ya dawo hayyacin sa,,,murmushi yayi kafin yace
lafiya,,ina fa lafiya kana nan ka antaya cikin tinanin jiddah koba haka bane nasan dai ita kadai keda wannadm matsayin, girgiza kai ammar yayi kafin ya fara,,hakanadm a yan kwanakin nan nakejin faduwar gaba kamar wani abu mara kyau zai sameni kuma tunanin jiddah yana fadomin cikin raina koda yaushe,,,numfasa wa abbas yayi kafin yace ni ina ga kamar rashinta a kusa da kaine ya kawo hakan amma ba abinda zai faru,,ya kamata ka kirata kaji lafiyarta,,,na fada maka na kirata amma wayar bata shiga anya lafiya kuwa ya kamata inji daga gareta dan ni wannan shirun nata bana lafiya bane dan yasan koshi bai kirata ba ita zata kirashi,,,

Ur's princes deejerh💝
[16/01, 18:48] khadija ahmad dija Marubuciya Barauniya ce Frien Din Hassn: ✨✨BA DON SHIBA✨✨

By Princes Deejerh
New Writer

Gaisuwa ta musamman gareku
Teemah sulfat
umma muhammad
noorul jannerh
asma baffa
khadeeajah candy
aneey lurv
aneesa didi

Page 5️⃣1️⃣ to 5️⃣6️⃣

WACE CE JIDDAH?

Malam salisu haifaffen garin zamfara ne a wani kauye da ake kira kiyawa,,matar sa ta aure guda daya ce tal halima tun auren saurayi da budurwa sai dai allah bai basu haihuwa da wuri ba,,har sun fara fidda rai da samun haihuwa allah maji rikon bayinsa sai ga halima da ciki,,lokacin da malam salisu ya samu wannan labarin ba karamin farin ciki ya shiga,,mutane ma na taya su farin ciki,,haka sukayi rainnn cikin nan da yake cikin mai laulayi ne sosai halima ta rame sosai tanajin ciwo a cikin jikinta amma bata nunawa saboda bata so hankalin malam ya tashi,,,a lokacin da cikin ya shiga watan haihuwa kuwa idan kaga halima sai ka tausaya mata domin ta kumbura ne ko tafiya dakyar take yinta,,,wataranar lahadi ta tashi da ciwon nakuda cikin dare,,,da sauri malam yaje ya kira ungozomar dake karban haihuwa a kauyen,,,koda suka zo tayi matukar galaiba ta domin ko numfashi bata iyayi sai da kyar,,,dabarun su na tsoffi ta fara mata amma haihuwa shiru azaba kawai take ci..malam yana daga kofar daki amma kamar shine ke haihuwan duk ya hada zufa,,har wajen asuba bata haihu a ba lokacin nan bambam cinta da gawa kalilan ne,,addu'a malam yayi cikin kofi sannan ya shigo cikin dakin,,ungozomar ce ta taimaka masa suka zuba mata a baki wani yana shiga wani na fitowa haka dai suka rinka bata har ta shanye,,,cikin abinda bai wuce minti biyar ba nakudar ta kara tasowa har tafi na farko azaba,,da sauri mallam ya fita ba zai iya jure kallonta cikin wannae halin ba,,,kamar jira take ya fita kuwa kan da ya fara fitowa sai kuma numfashin ta ya fara tsayawa,,,wani nishi tayi da karfi gaba daya yaron ya fado yana canyara kuka,,tunda halima tayi wannan nishin jikinta ya saki alamun ba rai,,daga waje malam ya fado cikin dakin ko ta yaron bai biba ya nufi inda halima take kallo daya ya mata yasan bata da rai,,,cikin tashin hankali ya fara girgiza ta amma inaaa rai yayi halinsa,,,,karar jin faduwar sa kawai ungozomar tayi wadda ke gefe rike da jariri tana jimamin mutuwar halima,,,,da sauri ta aje shi a gefe tayi waje ta kira makota,,,,kan kace me mutuwar halima ta zagayen garin kiyawa kowa nata jimami dan kuwa halima mutum ce ta gari ga son jama'a..masu kuka nayi masu addu'a nayi,,,malam kuwa tun faduwar da yayi bai farfado ba har sai da aka gama hada halima,,,Innalillahi wa inna ilaihir raji'un kalmar da yake ta maimata wa kenan kafin ya samu sassauci a cikin zuciyar sa...dakin da gawar take ya shiga ya tsugunna a gabanta addu'a yake kwararo mata yana nema mata rahamar ALLAH,,,,haka da aka binne ta ma sai da yayi mata addu'a yana hawaye kafin su dawo gida,,,,

haka aka cigaba da amsar gaisuwa har akayi addu'ar bakwai,,anan ne fa aka fara tunanin wa zaa ba muhammad sunan da malam ya sama yaron kenan,,,kowa yayi shiru alamun dai babu mai amasar sa,,,dan kuwa duk yan'uwan malam ne a wajen baida mahaifiya sai kannan uba da yayyen su,,,ita kuwa halima dama marainiya ce,,,,duk cikin su aka rasa wazai ce zai amshi yaron,,ganin haka da kawu iro ya gani,,yasa ya yanke shawarar aura mai ya'r sa TALATU kowa yayh1 na'am da hakan dan kuwa kawu iro duk shine babba a cikin su babu mai masa musu,,,,shima malam ba yadda zaiyi ne,,,a take a wajen akai komai aka gama abinka ga kauye,,,washe gari kuwa aka kawo amarya dakinta,,,

haka rayuwa ta cigaba da tafiya talatuwa bata nuna son muhammad sai malam na nan inko baya nan azaba yake sha kalakala a hannun ta,,,a haka suke rayuwa kullum tana tsanar muhammadu,,

lokacin da muhammadu ya cika shekara 25 tsufa ya kama mallam itama talatuwa haka amma duk da haka zuciyarta na nan da tsanar muhammadu,,shiko kyautata mata yake sosae domin yanzu sana'a yakeyi mallam ya bude masa provision a cikin kasuwar garin,,,ganin haka yasa talatu fara nema masa auren yar gidan kanwar ta ASABE,,,malam ya amince da hakan domin shi yana ganin talatu ba zata cuce shiba,,,

Asabe yarinya ce mara tarbiyya bata ganin kan kowa da gashi,,ba arabi ba boko sai ya yawon tallah da bin shagunan mutane,,,tuntuni take nunawa muhammadu so amma shi gani yake me zeyi da ita basu dace,,,kowa yasan asabe bata da mutunci indai zaka bata kudi tofah zata bika koma ina ne,,,dan bata dauki jikinta da daraja ba,,,da labarin auren ta da muhammadu ya shiga kunnenta kuwa farin ciki tayi mara iyaka,,,dama abinda ake nema ido rufe,,,

ba wani lokaci aka sa me tsawo  ba,,,akai auren muhammadu da asabe,,sai rawar jiki take..shiko kallon ta kawai a wulakance domin kuwa bata kawo mai yancinta,,,haka zamansu ya kasance kadahan kadaran da farko asabe kamar zaayi zaman lafiya da ita,,amma ta fara fito da mugayen halayenta bai isa ya sata abu tayi ba ga rashin kunyar tsiya,,gashi bata zama a gida kullum tana hanyar gidan bokaye,,ana haka ta samu ciki farin ciki sosai takeyi shima muhammadu ba'a barshi a baya,,,lokacin haihuwa allah ya bata da namiji akuma ranar ne mallam salisu yace ga garin ku nan,,,muhammadu ya shiga damuwa matuka da rashin mahaifin sa,,amma haka ya fawwala wa ALLAH komae,,ranar bakwai ranar ne sunan muhammadu yace ba zaayi taro ba kuma zai maida sunan malam akan yaron,,,nan fa asabe tayi tsalle ta dire ta ce ba zaa sama danta wannan sunan ba,,magana har gurin manya amma suka goyi bayan asabe,,,haka muhammadu ya hakura tasa ma yaron haladu,,,tun daga nan fa haihuwa ta bude ma asabe,,bayan shi yara uku ta haifa duk mata,,indo,rabi,da ma,u,,,,yara sun taso kamar uwar su basu da kunya duk abinda sukayi sai dai asa musu ido dae kuwa baa dukan ya'ya'n asabe,,,

ana haka ne allah ya hada malam da fatima kallo ya mata alla ya jarabce shi da kaunar ta,,fatima yarfulani tallan nono takeyi ita da yayyenta d,,,fatima yarinya kyakkyawa er kimanin shekara15 bata da hayaniya ko kadan ga hakuri,,,muhammadu bai tsaya wani jinkiri ba ya gabatar da kansa a wajenta da iyayenta,,,,duk sun amice dashi dan haka yaje ya fadawa kawu iro......

da kamar wuya....

Ur's princes deejerh💝
[16/01, 18:48] khadija ahmad dija Marubuciya Barauniya ce Frien Din Hassn: ✨✨BA DON SHIBA✨✨

By Princess Deejerh New Writer

Wannan shafin sadaukarwa ne a gareki ke kadai kiyi yadda da kike so dashi UMMYN YUSRA ina yinki irin sosai din nan😍

5️⃣6️⃣ to 6️⃣0️⃣

Haka kawu iro ya badawa idon shi kasa yace sam ba za'a yiwa ya'r sa kishiya ba,,a wannan lokacin muhammadu yaji sam ba zai iya bin maganar kawu iro ba,,,saboda haka yana tashi gidan malam idrissa ya nufa abokin baban sa tun na yarin,,ya kwashe komai ya fada masa...malam idrissa tsoho me dattako yace zai shige mai gaba ayi komai,,,,,haka kuwa akayi shida wasu abokanan sa su biyu suka je nema mai auren,,,aka gama komai cikin mutunci kowa na farin ciki aka tsaida rana sati uku masu zuwa,,muhammadu yayi matukar farin ciki da hakan...A lokacin da kawu iro yaji labarin cewa yayi lallai sai ya sakar masa yarinya,,tijara ba irin wanda beyi wa muhammadu ba,,,takanas ya taka har can gidan su inda itama asabe ke zuba ruwan rashin mutuncinta....shima da yake baban nata dakiki irin ta sai ya dora daga inda ta tsaya,,yana cewa lallai sai ya basa takardar ta,,,ai asabe najin zance saki jikinta yayi sanyi dan itafa har yanzu tana son mijinta,,ba kunya ba tsoron allah asabe tace itafa tana son mijinta,,,kawu iro tunda yaji tace haka ya saba babbar rigarsa yayi waje tare da fadin to ai shikenan tunda kin zabi zama da kishiya,,,

Kwanci tashi ba wuya a wajen allah yau saura kwana2 bikin muhammadu da fatima,,,asabe tayi tijarar tayi bala'in tayi rashin mutunci amma duk a banza malamai kuwa sunci iya nasu amma duk ba nasara hakan yasa ta hakura amma ta kudirta a ranta kowa ce aka auro to kamar ta shigo makabar ta ne dan har ta gama tanadin irin rashin mutuncin da zata mata..

Rana bata karya sai dai uwar diya taji kunya dan kuwa a yaune mutanen kauyen kiyawa suka shaida daurin auren muhammadu salisu da fatima hamisu jauro...muhammadu sai washe baki yake kallo daya zaka masa kasan yana cikin farin ciki,,,domin shi a cikin ranshi fadi yake yanzu ne yayi auren soyayya

Ko kafin magarib tayi har ankai amarya dakinta dake gefen dakin asabe,,,,iyayen fatima sunyi kokari sosai gurin tsara mata dakin ta duk da daki ne irin kauye,,amma hakan bai hana shi yin kyau ba‘’ana gama shirya komai mutane suka fara tafiya sai ya'n uwanta na jiki,,,fatima na lullube cikin koren mayafi ba abinda takeyi sai kuka fuskar nan tayi jajir,,,,duk hidamar nan da akeyi asabe bata nan ya'ya'n ta nacan gidan su,,,ita kuma tana can bin yawon malaman ta,,,,,kan kace me kowa ya watse gidan yayi tsiiit...a lokacin ne kuma muhammadu ya shigo dakin amarya fatima ya wuce tunda yasan har yanzu asabe bata dawo,,,amarya fatima na zaune bakin gado,,kanta a kasa...da dabara sai da muhammadu yasa ta saki jiki dashi,,,ledar hannun shi ya bude tsirene a ciki wanda yaji quli da kayan miya sai turiri yake,,,,dakyar fatima

taci dan ita nauyin shi takeji,,,shiko ko a jikin sa,,,haka ya lallabata,,,

wannan daren muhammadu yayi kwanan farin ciki a lokacin ji yake kamar bai taba aure ba dama,,,fatima kuwa tasha albarka dozen2,,,,

ita kuwa asabe koda ta dawo ko kallon sashen amaryar bata kalla ba tayi shigewarta dakin,,,a wannan daren asabe bata runtsa zirga zirga takeyi a dakin kamar kwancen hauka,,ji take kamar taje taita buga kofar dakin,,,,

washegari muhammadu ya tashi cikin farin ciki da kansa ya hada mata abin karya wa ya dibar mata nata ya diba na asabe ya kai mata dashi da abincin ko kallon arziki bai samu ba,,,shima bai biye mata ya fita ya koma dakin amarya fatima..

Haka rayuwa ta cigaba da tafiya fatima na kokarin ganin tayi ma asabe biyayya amma ita kuma bata gani  ita da ya'ya'n ta haka suke mata rashin mutunci kala kala,,,ba halin tayi magana haka zasu je kofar dakinta suyi wasa da kasa a kwaba da ruwa suyi kaca2 da wurin su kuma tashi su bar shi,,,haka asabe ke mulkinta son ranta a gidan ta wulakanta fatima yadda ranta yaso ita ya'ya'nta,,,fatima me hakuri ce koda yaushe sai dai ta shige daki tayi kukan ta ita kadai bamai rarrashinta..ko yan'uwanta sunzo bata iya fada musu,,,,ita kuma asabe bata tashi iskancin ta sai taga muhammadu bayanan .har jifanta take sa haladu yayi idan ta fito tsakar gidan,,,shiyyasa yanzu bata ma fitowan koda yaushe tana cikin dakinta,,

Ana cikin haka sai ga cikin ya bayyana a jikin fatima,,,muhammadu murna yakeyi kamar yanzun zaa fara haihuwa a gidan sa,,,,asabe kuwa ina wuta ta jefa fatima dan tsananin takaici da bakin cikin da take ciki,,,CIKI a jikin wannan ya'r mayun to wallahi wannan cikin ba zai taba zuwa duniya tayi alkawari hakan,,,mayafi ta zara tasa shafdeden silifas dinta ta fita a gidan kamar wata mahaukaciya,,,tayi alkwarin ko zatayi yawo tsirara sai ta salwantar da fatima da abinda ke cikinta,,,,

ANYA KUWA,,,,,

Muje zuwa wai mahaukaci ya hau kura😂😂

UR's princes deejerh💝
[16/01, 18:48] khadija ahmad dija Marubuciya Barauniya ce Frien Din Hassn: ✨✨BA DON SHIBA✨✨

By Princes Deejerh

New Writer

Wanga shafin sadaukarwa gareki MISS XERKs ke kadai kiyi yadda kike so dashi sannan kuma kici gaba da antayo mana HIDAYA NOOR

Page 6️⃣1️⃣
to 6️⃣5️⃣

Bata zame ko ina ba sai gidan malamin ta haka ta kwashe komai ta fada masa,,kulli magani ya bata sannan yace mata ta tabbar fatima ta tsallake wannan maganin idan har ta tsallake shi cikin zai zube kuma itada kara haihuwa har abada,,,cikin murna ta ciro kudi ta bashi,,,

haka ta kara kamo hanya buguzum buguzum tana tafiya tana sake saken mugunta cikin ranta,,koda ta isa ta tarar da fatima zaune bakin dakin,,yaranta kuma kowa ya tafi yawon shi,,ko kallon inda fatima take bata yiba ta shige dakinta,,,ita dai fatima baiwar allah tunda ta mata sannu da zuwa taji bata amsa mata ba taja bakinta tayi shiru,,daga karshe ma dakinta ta shige tayi kwanciyar ta

asabe na daki amma sake sake take yi a ranta na yadda zata zuba wannan maganin a kofar dakin fatima,,,lekawa tayi taga tsakar gidan ba kowa komawa daki tayi ta dakko maganin sannan ta fito ta fara tafiya a hankali har takai kofar dakin fatima da take can daki tana barci bata san wainar da ake toyawa ba,,,,bude kullin maganin tayi sannan ta barbada shi a duk kofar dakin sannan ta juya ta koma tana murmushin nasara...

kiran sallar la'asar ne ya farkar da ita daga barcin da takeyi buta ta dauka domin zagawa bandaki kafin tayi alwala,,bata ko kalli kofar dakin ba ta tsallake tayi wuce,,,tana wucewa taji kamar an tsikare a mararta bata kawo komai ba a ranta ta shige bayi,,,,ta tsugunna da niyyar yin fitsari a maimakon ya fito sai jini taga yana fita kamar anbude famfo,,,cikin tashin hankali ta mike da sauri amma kuma sai taga jinin nabin cinyoyinta ga wani murdawa da mararta keyi,,dakyar ta lallaba ta fito ta koma daki duk inda tabi sai jinin ya zuba...
i
asabe na daga kofar window din dakinta tana ganin komai farin ciki ne ya kamata ganin aikin ta yaci,,,murmushin mugunta tayi tana fadin ni asabe wazai ja dani ya kwana lafiya ballantana wata karamar alhaki wai fatima kinta gani kenan keda haihuwa har abada sai dai kiga mata nayi...(nidae nace ta allah bata kiba asabe🤨🤨)

muhammadu kamar yasan abinda ke faruwa yau yaji yana son dawowa da wuri haka ya kamo a

er kekensa ya taho gida,,,dakin asabe ya fara shiga,,kallon da yaga tana mai ne yasa shi kara kallonta,,ganin zai dagota ne yasa ta fara magana,,sannu da zuwa ai yanzu na dawo daga wajen kawu yace yana gaesheka,,,toh kawai yace ya fita ya nufi dakin fatima,,,asabe bata so ya dawo yanzux tasone jinin ta yayi ta zuba har azo a samu gawarta,,,,(MUGUWA😡)

jinin da ya gani kofar dakin ne ya sashi karasa wa da sauri cikin dakin inda anan ne yaga tashin hankali,,,kwance take cikin jini shame shame sai numfashin ta dake fita kadan kadan,,,cikin tashin hankali ya karasa inda take tare da tallafo yanayin daya ganta ne yasa shi fashewa da kuka,,,,da yaga haka bazata mai ba sai ya sabeta a kafada yayi waje da sauri,,haka ya rinka ratsawa har ya isa da ita karamin asibitin dake garin,,,da sauri aka amshe ja aka shigar da ita ciki,,,shi kuma ya koma gefe yana zirga zirga tare da tinanin me ya jawo mata hakan shidai yasan lafiya lau ya barta kafin ya fita,,,,

sai dai aka share awa biyu a kanta da kyar likitan ya samu ya tsayar da jinin dake zuba sannan aka mata allurar barci,,,likitan na fitowa muhammadu ya taso da sauri yabi bayan shi sai da ya shiga office din likitan kafin ya fara tambayar shi halin da fatimar ke ciki,,,,bayani ya fara cikin nutsuwa,,,,gaskiya duk iya dubarwa da mukayi bamuga wata matsala ba da har yasa wannan jinin zuba ba,,,sannan kuma har yanzu cikin nanan bai fita ba sai dai zaka bari zuwa gobe sai a sallameku,,,farin cikin da muhammadu yaji a lokacin bai misaltuwa,,,gidan su fatima yaje ya fadawa mamanta abinda ke faruwa tare suka tawo asibitin sannan shi kuma ya koma gida dakko kayan da zasuyi amfani dashi,,,

sai da fatima tayi kwana2 a asibiti jiki kam alhamdulillah taji sauki sosai,,ba wanda baije gaisheta ba amma banda asabe,,,,dan tunda taji ance fatima ta samu sauki take cikin takaici da bakin ciki

haka sanda fatima ta dawo duk makota na shigowa yi mata ya jiki asabe naji tana zaune a dakin tana fama da bakin cikin da ya cika mata zuciya,,,

haka rayuwa ta cigaba da tafiya cikin fatima na girma amma daga ita sai muhammadu suka sae tanada ciki kowa yana tinanin cikin ya zube ciki kuwa harda asabe,,,wadda keta murna shiyyasa yanzu kota kanta bata bi
ita a tinanin ta ai tariga ta gama da ita

🤣🤣🤣Asabe sai dai kiji kukan baby aradu

Pls kuyi hakuri da wannan

Ur's princes deejerh💝

[16/01, 18:48] khadija ahmad dija Marubuciya Barauniya ce Frien Din Hassn: ✨✨BA DON SHIBA✨✨

By Princess Deejerh
New Writer

Ina kuke 6ters na kwarai wannan shafin sadaukar wa gareku ina yinki irin totally dinnan
Aisha mohammed sani(Zayeeshart)
My Nusaiba mu'hd auwal(Nusy bea)
Ruqayyerh tertherr risqua(er kanwata)
Umma muhammad(Ummu aiman)
Pharteemah Ahmad(teemah sulfat)
Phertymah harun(mommy kd)

Ga masu son shiga group dina BA DON SHIBA FANS CLUB ko kuma PRINCES DEEJERH NOVEL sai ku tuntubeni ta wannan numbers
08104609894
09061274993
08060972795
07033851935

Page6️⃣6️⃣to7️⃣0️⃣

Haka fatima da muhammadu suka cigaba da rainon cikin da ba wanda yasan dashi domin kuwa kullum da hijab take kuma dama cikin nata bamai girma bane

Ranar wata talata da safe fatima ta fara nakuda bata sha wata wahala da kanta ta santalo lafiyayyar ya'rta mai kama da larabawa dan kuwa fara ce jajir babu ta inda ta bambamta da uwartt,,,farin ciki kuwa gurin muhammadu bai irguwa da kanshi yaje har gidan su ya taho da kanwar innarta ita tayi mata komai ta yanke ma jinjirar cibi ta wanke ta tass sannan aka nadeta a wani farin towel,,sannan ta hada ma fatima ruwan itama da kanta tayi mata wankan,,kafin ta dumama mata tuwaon dawa ta kawo mata,,,idan kaga fatima ba zaka ce itace ta haihu ba dan kuwa lafiyarta kalau ita da jaririyarta,,,muhammadu ne ya shigo dakin hannun sa rike kayan tea da siyo mata gurin ya nufa tare da daukan jinjirar fuskar nan fal farin ciki da annushuwa,,sai da yayi ma yarinyar addu'a kafin yayi mata huduba da suna HAUWA'U JIDDAH,,,fatima tayi matukar farin ciki da yasa mata sunan innar ta,,,sai a lokacin mutane suka fara shigowa gidan

suna yi mata barka suna santin kyan yarinya,,,ita dai saidai kawae tayi murshi idan mutane na tambayar ta wai dama ciki gareta,,,ko en uwanta da suka zo mamaki suka rinka yi tare da godema allah,,,

shigowarta kenan gidan taga mutane wasu na fitowa daga dakin fatima wasu na shiga ga kuma en uwanta zazzaune a kofar dakin,,,mamaki takeyi tow meye akayi haka da har dangin mayyar can suka zo suka wani cika musu gida da hayaniya inama mutuwa shegiyar can tayi ai wlh da sai ta kira masu kidan kwarya sun buga mata ta cashe,,,sallamar muhammadu ce ta katshe mata tunanin da takeyi ko amsar sallamar bata yiba ta tsaya kallon shi ganin sai wani washe hakora yake,,,katse yayi tare da fadin amm... asabe munfa samu karuwa yau a gidan nan,,,,be tsaya jin me zata ceba ya cigaba da fadin dazu fatima ta haihu mun samu ya' mace jiddah,,,tana zaunau a kan kujera ertsugunne amma sai data wuntsila tare da bajewa a dakin tayi zaman yan bori,,,cikin zaro ido tace wata fatiman,,,hanyar waje yayi yana fadin fatima nawa garemu a gidan tareda ficewa,,,yana fita ta zube a kasa burgima ta fara a tsakar dakin ta rasa inda zata tsoma ranta kawai saita fashe da kuka da wannan ranar ai gara mutuwar ta malam ya cuceni ya yaudareni,,kuka takeyi kamar karjmar yarinya,,,fatima ce wai ta haihu ta kara maimaitawa wallahi sai naga bayanta ita da shegiyar ya'r tata,,,

Haka akayi suna cikin kwanciyar hankali rago biyu manya manya muhammadu ya yanka mata bayan kaya da ya dinka mata itama jiddah ya saya mata kaya sosae ga kuma wanda dangin fatima suka mata komae dae alhamdulillah,,,tun mutane na tambayar fatima ina kishiyar ta take har suka bari,,dan asabe bakin cikin ta take nunawa kiri kiri ba abinda ta taba ko taci wanda ya danganci haihuwar fatima kuma bata fasa bin malaman ta daka ganta kasan bata da kwanciyar hankali...

taron suna ya watse kowa na sam barka fatima ta cigaba da renon yarta itada muhammadu,,,asabe saidai ido dan ita kadai tasan tsiyar data shuka kuma tasadm tabbas wannan sai tayi nasara domin wannan ba irin wancan bane...

Wata ranar sati muhammadu ba zai taba manta ta ba da kuma iyayen fatima da en uwanta,,,a safiyar da aka nemi fatima sama ko kasa aka rasa ba inda baa je nemanta ba a kauyen kiyawa har makotan su amma ko sawunta ba'a gani ba,,muhammdu suma yayi sai da ya kusan awa biyu kafin ya farfado ,,,yana farfadowa ya tashi tare da nufar kofar gida mutane suka rike shi amma ina turjewa yakeyi yana fadin abar shi yaje ya nemo fatimar sa,,,basu kara shiga tashin hankali ba sai da jiddah ta fara kukan yunwa aka rasa yanda zaayi innar fatima ce ta amshi yarinyar tana jijjigata amma ko alamun yin shiru batayi,,,fashewa da kuka kowa yayi ganin muhammadu na kuka wiwi kamar mace,,a yau asabe tayi rawa tayi juyi tayi hawayen farin ciki burinta ya cika,,dama sabon malaminta yace kurciya zaa mata itada dawowa garin kiyawa har abada,,,

Tsawon sati biyu kenan ba fatima ba labarinta jiddah kuwa tana gurin innar fatima itake renonta

a yanzu kudi muhammadu ya bada isassu aka siyo madarar jarirai kuma da akayi saa tanasha sosae,,,muhammadu a yanzu rayuwa kawae yake domin kuwa asabe saida ta mallake shi tsab komai sai idan ita tace yayi tsoronta yake matuka yanzu,,kudi take amsa a gunsa koda yaushe tana wadakarta ita da yaranta shiko ya zama konko yanzu

BAYAN SHEKARA DAYA

a yanzu kam muhanadu baida komai asabe ita da ya'ya'nta sun gama cinye kudin shi tsab yanzu shagon da yake zuwa ma ankwace saboda rashin biyan kudin haya,,,

jidda kan yanzu shekarar ta daya tana gudun ta koina har anyaye ta,,yarinya me kyau me shiga rai ga gashinta dogo baki sidik daka ganta kasan jikar fulani ce,,,

A wannan lokacin ne kuma muhammadu ya samu aiki a garin kaduna na gadi saboda haka duka zasu tafi harda asabe da yaran yaso yabar jiddah amma asabe ta rura wuta sai da ya amsota,,,

haka suka tattara suka koma garin kaduna da zama a gidan suke zaune a BQ a lokacin ne jiddah ta fara shiga matsalar rayuwa duk da kuwa kankantar ta amma haka asabe ke mata mugunta kalakala,,ana cikin haka ne malam muhammadu ya sayi wani dan karamin gida da kudin da yake ajiyewa suka koma can,,,sun koma ba dadewa malam muhammadu ya fara ciwon ajali kwana2 yayi yace ga garin ku nan,,,asabe tayi kukan mutuwar shi nadan lokaci ta share ta cigaba da rayuwas itada yaranta,,,

mutuwarsa  tasa jidda kara shiga matsalar rayuwa asabe sai taga damar bata abinci yawo take kamar almajira a cikin unw a lokacin shekarta 12 su rabi kam a lokacin anza entayi galan ana kawowa inna asabe kudi tana amshewa tana murna

ana cikin irin wannan rayuwar ne ALLAH ya jefo ammar cikin rayuwar jiddah ganin farko daya mata yaji ta shiga ranshi ga kuma tausayinta da yakeji saida ya tuntubi makota suka bashi labarinta tofa tunda ga wannan rana ammar ya fara kula da jidda da kansa ya sata a makaranta ya dinka mata uniform,,shike bata duk wata kulawa,,,inna asabe zata mai rashin mutunci ya nuna mata nashi rashin mutuncin yafi nata haka nan ta hakura badan ranta na so,,,,,

CIGABAN LABARI ku biyo a next page

Ur's princes deejerh💝
[16/01, 18:48] khadija ahmad dija Marubuciya Barauniya ce Frien Din Hassn: ✨✨BA DON SHIBA✨✨

By Princes Deejerh
New Writer

AMEENTA WRITERS ASSOCIATION🤝

Page 7️⃣1️⃣to 7️⃣5️⃣

CIGABAN LABARI

Tun dawowar inna asabe daga wurin bokan ta ta kasa zaune ta kasa tsaye.domin kuwa a yaune take son ta gama duk wani mugun kullin ta a kan jiddah ta rasa yadda zatayi ta shiga dakin dabara ce ta fado mata dakin ta shiga ta dauko kudi sannan ta nufi dakin jiddah.kwance ta tarar da ita amma ba bacci take ba tana ganin shigowar inna asabe ta mike tare da fadin sannu inna ashe kin dawo,eh tace‘’sannan ta fara fadin yauwa jiddah dama so nake na aikeki gidan mutuniyar ki maman salaha ki amso min kayan na 100.

to tace sannan ta dauki hijab ta zira takalmi sannan ta fita.

fitar ta keda wuya inna asabe ta bankade er yagalalliyar katifar dubawa tayi taga ba wani rame a wajen kuma idan tasa a haka zaa gane wuka ta dauko ta samu bakin katifar ta bula sai da taga yayi zurfi sannan ta barshi ta ciro layar dake daure a habar zanin ta ta tura ciki kara komawa dakin ta tayi ta dauko zare da allura ta dinke bakin wajen sai da ta kalla dakyau ta ga ba wani alamun da za'a gani sannan tayi murmushin mugunta tace‘’jiddah na gama dake kodah wannan na barki na rama bakin cikin dana kunsa na uwarki da naki,mikewa tayi ta fice daga dakin.

AMMAR ne zaune a daki shi kadai yana hutawa yau bashi da lecture ya kara kyau ya kara fari fatar nan sai glowing take saboda hutu da amfani mayuka da alamu dai kasar india ta amshe shi,wani dan karamin passport ne a hannun shi tun dazu ya kura masa ido yana duk sanda ya kalli ta jikin hoton sai gaban shi ya fadi,wayar sa dauko domin kiran ta kamar dai ko yaushe yauma a kashe take,

wurgi yayi da wayar cike da takaici yana fadin why jiddah zaki kashe waya bayan kinsan zan nemeki.

Abbas ne ya shigo dakin tare da fadin kaga na jiddah ba da kanka asare idan aka ga bacin ranka to jiddah aka tabo.

kallon shi ammar yayi kafin ya kaude kai yana fadin saura 2 years na gama karatuna gaskiya yayi min nisa inaso insan halin da jiddah ke ciki nifa ina ji a jikina wani abu na faruwa.

abbas ne ya katse shi tare da fadin "to yanzu me kake nufi kenan?uhm idan kayi hakuri kamar fa gobene yanzu 3years kenan da zuwan ka 2years zai maka wahalan karasa,ka daina sa tunani a ranka jiddah tana nan lafiya.

kallon shi ammar yayi tare da fadin ALLAH yasa hakan.

Ba wani dadewa tayi ba ta dawo hannun rike da kayan miya dakin inna asabe ta nufa ta bata,har zata juya sai kuma ta dawo tana fadin"kawo in gyara,A'a kibar shi kawae jeki cigaba da baccin ki..

dakin ta ta koma ta cire hijabin har zata kwanta ta tuna gobe suna da test,jawo jakar ta tayi sannan ta fara duba littafan ta sai da ta kwashe kusan 1hr sannan ta ajiye ta kwanta kafin la'asar tayi.

Kiran sallah la'asar ne ya farkar da ita tana son tashi tayi sallah amma ta kasa gaba daya jitayi gabobin jikinta na saki.

komawa tayi ta kwanta tana fadin anjima nayi,

haka ya faru a lokacin sallar magrib.

inna asabe ce zaune da su rabi duk cikin su bamai kayan arziki HALADU kuma na gefe yana cin abinci.

inna asabe tace"Rabi dake da asiya ku zabar ma jiddah kaya a cikin naku amma fa duk kananu kamar dai na jikin ku din nan,to suka ce tare da mikewa dan sun riga da sun san manufar hakan..

kallan kayan take daya bayan daya sanda inna asabe takai mata kuma tana fadin wai nata ne su rabi suka bata.

amsa tayi kawai amma har cikin ranta kayan basu mata ba amm kuma ta kasa musawa....

Ur 's princes deejerh💝
*✨✨BA DON SHIBA*✨✨

*By Princes Deejerh*
*New Writer*

*AMEENTA WRITERS ASSOCIATION*🤝

*Page*7️⃣6️⃣*to*8️⃣0️⃣

Inna asabe tana ganin *jiddah* ta amshi kayan ta koma daki tana murna ita da 'ya'yan ta.

